# DEUTSCHE WELLE
# JI KA KARU

## Tuntuɓar juna tsakanin addinai: Haɗin kan mutanen Sodangi
## Kashi na biyu: Cuɗe ni in cuɗe ka


Wanda ya rubuta: Romie Singh
Wanda ya tace: Katrin Ogunsade, Naïma Guira
Wanda ya fassara: Ɗanlami Bala Gwammaja


**'Yan Wasa:**

| | |
|---|---|
| Tafida: | ɗan shekara 17 |
| Dauda: | ɗan shekara 17 |
| Ɗanjuma: | ɗan shekara 16 |
| Shugabar makaranta (Madam Titi): | 'yar shekara 48 |
| Baban Tafida: | ɗan shekara 50 |
| Layla: | 'yar shekara 16 |
| Hassan: | ɗan shekara 12, ɗan'uwan Layla |
| Fada Bana: | ɗan shekara 49, kawun Dauda |

**MAI GABATARWA:**
Jama'a, barkanmu da sake saduwa da ku a cikin shirinmu na "Ji Ka Karu" inda a yau za ku saurari kashi na biyu daga cikin goma na wasan kwaikwayon nan mai suna "Haɗin kan mutanen Sodangi", wanda a cikinsa za ku ji yadda addini da siyasa suka haddasa zaman doya da man ja a tsakanin al'ummomi guda biyu, da kuma wasu maƙwabtan juna biyu, da kuma tsakanin wasu matasa guda biyu, wato Dauda da Layla. Yanzu dai sun shiga sabuwar shekarar karatu tare da abokansu. A cikin shirin namu na yau mai suna "Cuɗe ni in cuɗe ka", Tafida ya fuskanci wani babban ƙalubale a makarantarsu, sannan kuma babansa yana matsa masa lamba. Layla da Dauda sun haɗu da wasu matsaloli a gida. To, sai ku biyo domin jin yadda za ta kaya.

**Fitowa ta 1: A Kwalejin Zumunta**
Shugabar makaranta, Dauda, Tafida, Ɗanjuma, Ɗalibai

**SHUGABAR MAKARANTA:** Ɗalibai, kun tashi lafiya?

**ƊALIBAI:** Lafiya lau.

**SHUGABAR MAKARANTA:** To, ina yi muku barka da dawowa Kwalejin Zumunta. Bari na gabatar da kaina, musamman saboda sababbin ɗalibai. Sunana Madam Titi, kuma ni ce shugabar wannan kwalejin. Yau shekara goma ke nan da buɗe wannan makaranta. Wannan kalma ta zumunta ita ce ginshiƙin sunan wannan makaranta tamu, sannan kuma saƙon da wannan suna ya ƙunsa shi ne: "cuɗe ni in cuɗe ka", wanda hakan wani ginshiƙi ne a cikin al'adunmu na Afirka. Ba don kasancewarmu al'umma ɗaya ba, to da mun zauna cikin rauni da kaɗaici. Duk abin da muke yi muna yi ne saboda al'ummarmu, don ita ce makaranta a gare mu, ita ce tushenmu, ita ce take kyautata 'yan'uwantakarmu, da kuma yanayin zamantakewarmu,...

**DAUDA:** Don Allah ka daure ka gaya wa wannan kawun nawa wannan magana da yake ganin shi mai tsarki ne. Shi fa gani yake kamar Allah ne ya aiko shi duniya.

**TAFIDA:** Kai Dauda! Wannan kawun naka fa fada ne na ƙwarai.

**DAUDA:** A'a! Me ya sa kake kare shi ne, Tafida? Ka fa san so yake ya hana mu mu wataya, wai shi dole sai ya mai da ni fada!

**SHUGABAR MAKARANTA:** ...wanda hakan shi zai sa mu zama cikakkun mutane. A yanzu sai mu miƙe don mu rera taken wannan makaranta! To mu fara!

**MAI BA DA LABARI:**

To da ma dai Kwalejin Zumunta makaranta ce ta musamman, shekara biyu kawai ake yi a cikinta. Amma a cikin shekarun nan biyu kacal, akan fahimci al'adu da ɗabi'u da kuma addinan juna. Duk da cewa suna zaune ne a gari ɗaya, wannan bai sa sun fahimci addinan junan ba, ko da yake da yawa daga cikinsu suna zaton sun sani. Amma fa kuskure suke tafkawa, musamman ta yadda sukan ɗauki ire-iren zantuttukan da ake yi a gari barkatai da kuma irin abubuwan da sukan kwaikwaya daga fina-finai da suke gani. Manufar kafa Kwalejin Zumunta ita ce don ta haɗa kan jama'a ta ilmantar da yara matasa yadda za mu fahimci juna da kuma dasa haƙuri da mutunta junansu.

**SHUGABAR MAKARANTA:** To ɗalibai, yanzu kuma mu yi addu'a.

**GABA ƊAYA:** *Ya Ubangiji muna roƙonka zaman lafiya mai ɗorewa, don zukatanmu su samu nutsuwa.*
*Ka ba mu zaman lafiya ya Ubangiji, don mu shuka alheri, mu faɗi alheri, mu kuma aikata alheri gaba ɗaya.*
*Ka ba mu zaman lafiya ya Ubangiji, don mu zama masu dangana da godiya da irin baiwar da ka yi mana.*

*Ka ba mu zaman lafiya ya Ubangiji, don mu samu mu ci moriyar baiwarka a fafutukar da muke ta rayuwa.*
*Ka ba mu zaman lafiya ya Ubangiji, ka kuma ba mu juriya da haƙurin zama da juna, ko ma sami rahamarka da jin-ƙanka.*
*Ka ba mu zaman lafiya ya Ubangiji, don mu yi rayuwa mai ma'ana, kuma hasken rahamarka ya kore dukkan duhu.*

**MAI BA DA LABARI:**
Kullum da safe sai an yi addu'a wadda za ta dace da kowane addini. Wato dai addu'a ga Ubangiji da kowa ya yi imani da shi, har ma da mutane irinsu Tafida waɗanda ba su yi imani da wani Ubangiji ba.

**SHUGABAR MAKARANTA:** *Ka ba mu zaman lafiya ya Ubaniji, a matsayinka na mahaliccinmu, don bayinka dake doron ƙasa su zama al'umma ɗaya. Amin.*
A bisa tsarin manufofin wanda ya kafa wannan makaranta, wato kakanmu Maigida Sulaimanu Bahago, yanzu zan sanar da sunan shugaban ɗalibai maza da kuma shugabar ɗalibai mata, su ne za su dinga zama wakilan da za su dinga sa da ku da ni. Waɗannan shugabanni su ne: Layla Umar da kuma Dauda Dembele! … Ku zo ku karɓi bajonku na shugabanci.

**ƊANJUMA:** To yaya aka yi haka ne, Tafida, na san za ka ji ba daɗi ko? Na ɗauka kai da za a naɗa!

**TAFIDA:** Ba kome Ɗanjuma. Ka san ni ba ni da wani kawu fada mai faɗa a ji!

**ƊANJUMA:** Kai! Kada ka bari wannan abin ya shiga tsakaninka da Dauda. Kar ka manta har yanzu muna tare, mu ne fa manyan yaran Kwalejin Zumunta, ko ba haka ba?

**TAFIDA:** E, haka ne!

**MAI BA DA LABARI:**
To, duk sai jikin Tafida ya yi sanyi. Tabbas kamata ya yi a ce shi aka naɗa a matsayin shugaban ɗalibai, don ya girmi Dauda da shekara guda, kuma ga shi sakamakon jarrabawarsa ya fi tasa kyau. Bai san dalilin da ya sa aka tsallake sunansa ba. Babansa ma da ya ji, abin bai yi masa daɗi ba.

**Fitowa ta 2: A gidan su Tafida**
Baban Tafida, Tafida

**BABAN TAFIDA:** Amma fa Tafida, na ɗauka na fito fili na yi wa shugabar makarantar nan taku bayani cewa, ya kamata fa idan an tashi irin wannan harka a dinga tsar ma mutane irinmu waɗanda ba su yarda da kowane addini ba, don mu za mu dinga yi wa kome kallon tsanaki. Mu fa muna cikin harkar nan ne don mu gyara wa duk wanda yake ganin akwai Ubangiji zama, mu kuma tabbatar da aƙidarmu ta 'yan ba ruwanmu da addini. Wannan shi ne abin da ƙasarmu take buƙata a halin yanzu!

**TAFIDA:** Haba Baba, ai bai kamata a ce ka yi ƙoƙarin cusa wa Madam Titi ra'ayi ba, ashe shi ya sa ma ba a zaɓe ni a matsayin shugaban ɗailbai ba.

**BABAN TAFIDA:** Zancen banza! To tsaya, wa ma aka zaɓa a matsayin shugabar ɗalibai mata?

**TAFIDA:** Ummm, Layla Umar ce.

**BABAN TAFIDA:** Haka ne! Layla? Ummm…e to. Ka san Layla yanzu ta fara zama 'yar duniya. Yaya na ga ka canza fuska? Ina fatan dai ba sonta kake ba. Yau ga abin mamaki, ai kuwa bai…

**TAFIDA:** A to, me zai hana? Don ka ga ita Musulma ce? Ai da ka san haka ne da ba ka sa ni a Kwalejin Zumunta ba, tun da ba ka so ina cuɗanya da wasu mutane!

**MAI BA DA LABARI:**
Daga wannan magana sai baban Tafida ya fice daga ɗakin a fusace. Ko me ya fusatar da shi, oho? Can kuma, ga Layla suna sa-in-sa da ƙaninta Hassan, wanda shi wannan naɗin da aka yi mata na shugabar ɗalibai mata, bai burge shi ba.

**Fitowa ta 3: A gidan Malam Isma'ila**
Hassan, Layla

**HASSAN:** To, wai Layla, me ya sa makarantar nan taku ake naɗa shugaban ɗalibai namiji da kuma shugabar ɗalibai mace?

**LAYLA:** Don mu ma a dinga damawa da mu mana, Hassan. Ai kamata ya yi a dinga daidaita mata da maza, wannan shi ne dalilin.

**HASSAN:** Ai maza ne ya kamata su zama shugabanni, ba ku ba. Ku mata aure za a yi muku ku samar da zuriya. Duk wani zancen ilimin mata ɓata lokaci ne kawai.

**LAYLA:** Kai, ni kana ɓata min lokaci! Ba ni wuri na tafi wajen motsa jikina ma.

**HASSAN:** Ai bai kamata ba. Mata Musulmi ba sa buɗe fuskarsu haka a fili!

**LAYLA:** Ka ga Hassan, ina sa hijabi. Abin da ake so shi ne na rufe kaina kawai, ba wai sai na rufe fuskata gaba ɗaya ba. Ban san irin abin da suke koya muku a wannan makarantar ba, amma mata Musulmi na iya yin wasannin motsa jiki.

**HASSAN:** Ai ba a yarda mace Musulma ta buɗe jikinta a gaban waɗanda ba Musulmai ba. Wato don kin ga Baba ba ya nan shi ne kike jin ....

**LAYLA:** Ai Baba ya san da tsarin makarantar. In kuma kana da wata magana ce sai ka je ka sami Madam Titi, ita ce shugabar makarantar. Ni abin da malamaina suka koya min shi nake yi.

**HASSAN:** Tsaya ni! Tsaya ni, Layla, ni ma za ni.

**MAI BA DA LABARI:**
Shi kuwa Dauda yana can cikin farin ciki. Ga shi shugaban ɗalibai, kuma ɗan babban mutum. Ga kawunsa, wato Fada Bana, wani mai faɗa a ji ne a tsakanin al'ummar Kiristoci na garin Sodangi. Sai dai shi wannan fada ba ya wata rawar jiki da duk wannan matsayi da ɗan yayan nasa ya samu.

**Fitowa ta 4: A gidan Fada Bana**
Fada Bana, Dauda

**FADA BANA:** Ka ce kawai ba ka son wannan muƙamin, Dauda! Me ya sa kai kome sai ka fito fili? Ba ka ganin ni fada ne? Don Allah ya kamata ka kula fa!

**DAUDA:** Don Allah, Kawu. Umm... yauwa! Ga su Ɗanjuma da Tafida ma sun zo don mu je mu yi wani *party* na murnar zamana shugaban ɗalibai. Ai ma iya tafiya ko?

**FADA BANA:** Kai Dauda, yawon nan ya isa haka fa! Ni na fi son ka zauna a gida ka mayar da hankalinka a kan nazarin *bible*. So muke mu fara koya ma dabarun zaman rayuwa, ko ma na yadda za ka zama mai wa'azi!

**DAUDA:** Haba Kawu! Ni fa…ni fa ba na so! Ni ba na jin zan zama wani mai wa'azi.

**FADA BANA:** Wannan zancen banza kake. Ai ba ka yi hankalin da za ka iya yanke wannan hukuncin ba. Haba ɗana! Ai aikina ke nan, na shiryar da kai zuwa ga hanyar Ubangiji.

**DAUDA:** Mhmmm, Kawu. Ka ga, yau fa ƙarshen sati ne, kuma ga shi na zama shugaban ɗalibai. Manyan yaran Zumunta suna so mu je mu wataya fa.

**FADA BANA:** Su...su wa? Tun yaushe kuke...?

**DAUDA:** Haba Kawu, su ne fa kawai! Tare muke bal, kuma tare muke wasan motsa jiki...

**FADA BANA:** Ku kuma tafi kulob tare ba! To, ka sani dai ba ka da damar ka sha giya don shekarunka ba su kai ba. Kada ka kuskura ka bari na....

**DAUDA:** Haba Kawu, ai na sani! Wajen shan shayi ne fa kawai. Shayi da lemo fa kawai muke sha, sai kuma karta da muke yi. Shi ke nan fa, Kawu!

**FADA BANA:** To, ai za mu je ƙauye cikin ƙarshen wannan satin. Lalle sai mun kafa maka wasu sabbin dokoki. Ku je!

**MAI BA DA LABARI:**

Daga nan ba su zame ko'ina ba sai kulob ɗin "Mu sheƙe ayarmu" inda suka sha hirarsu da 'yam mata kamar yadda suka saba, suka kuma yi wasan karta. Amma duk da haka, akwai wani abu da ya tsaya wa Tafida a rai, wato Dauda a matsayin shugaban ɗalibai, suna aiki kafaɗa da kafaɗa da kyakkyawar yarinyar nan Layla a matsayinta na shugabar ɗalibai mata! Haka zuciyarsa ta yi ta tafasa. Zai iya haƙura da wasan bal ɗin da yake yi, da kuma zamana ɗaya daga cikin manyan yaran Zumunta, in har za ta zama tasa. Amma ina! Hakan ba za ta yiwu ba. Kallon da yake mata daga nesa a wajen motsa jiki ko a filin guje-guje shi ne rabonsa kawai! Kusan ko da yaushe ɗan'uwan nan nata Hassan, yana laɓe yana lura da ita.

**MAI GABATARWA:**

Wannan shi ne ƙarshen shirinmu na yau na "Ji Ka Karu" a kan "Haɗin kan mutanen Sodangi". Waɗannan yara matasa sun fara fahimtar cewa shugabanci a makaranta dabam yake da na gida. Jan ragamar iko ba abu ne mai sauƙi ba. Jama'a sai ku biyo Dauda mu a kashi na uku a cikin shirinmu domin jin yadda Dauda ya gano irin farin cikin da ya yi lokacin da suke aiki da Layla. In kuna neman sauraron wannan shirin ko kuma aiko da tsokaci, kuna iya tuntuɓarmu ta adireshinmu na yanar gizo, wato www.dw-world.de/Ibe.